<u>Hausa - Agape Littattafai - God's Love Letter Scriptures</u>

Yahaya 15:9 Kamar yadda Uba ya ƙaunace ni, haka ni ma na ƙaunace ku. To, ku zauna cikin ƙaunar da nake muku.
Ishaya 43:1 Ya Isra'ila, Ubangiji wanda ya halicce ku ya ce, "Kada ku ji tsoro, na fanshe ku. Na kira ku da sunanku, ku nawa ne.
Irmiya 1:5 "Na san ka tun kafin a yi cikinka, Na keɓe ka tun kafin a haife ka, Na sa ka ka zama annabi ga al'ummai."
Yahaya 15:16 Ba ku kuka zaɓe ni ba, ni ne na zaɓe ku, na sa ku ku je ku yi 'ya'ya, 'ya'yanku kuma su tabbata, domin kome kuka roƙi Uba da sunana yǎ ba ku.
3 Yahaya 1:2 Ya ƙaunataccena, ina addu'a kǎ sami zaman lafiya ta kowace hanya da kuma lafiya jiki, kamar yadda ruhunka yake a zaune lafiya.
Ishaya 43:4 Zan ba da dukan al'ummai don in ceci ranku, Gama kuna da daraja a gare ni, Gama na ba ku girma, ina kuma ƙaunarku.
Irmiya 31:3,4 Ubangiji ya bayyana gare ni tun daga nesa cewa, "Ya Isra'ila, budurwa! Na kusace ki da madawwamiyar ƙaunata, Ba zan fasa amintacciyar ƙaunata a gare ki ba. Zan sāke gina ki, Za ki kuwa ginu, Za ki ɗauki kayan kaɗe-kaɗe, Za ki shiga rawar masu murna.
Yusha'u 11:8 "Ƙaƙa zan iya rabuwa da ke, ya Ifraimu? Ƙaƙa zan miƙa ki, ya Isra'ila? Ƙaƙa zan maishe ki kamar Adma? Ƙaƙa zan yi da ke kamar Zeboyim? Zuciyata tana motsawa a cikina, Juyayina ya huru.
Yahaya 3:16 "Saboda ƙaunar da Jehovah ya yi wa duniya har ya ba da makaɗaicin Ɗansa, domin duk wanda ya gaskata da shi kada ya hallaka, sai dai ya sami rai madawwami.
Ishaya 49:15,16 Saboda haka Ubangiji ya amsa ya ce, "Mace za ta iya mantawa da jaririnta, Ta kuma ƙi ƙaunar ɗan da ta haifa? Ya yiwu mace ta manta da ɗanta, To, ni ba zan taɓa mantawa da ku ba. 16 Ya Urushalima, ba zan taɓa mantawa da ke ba, Na rubuta sunanki a gabana.
Ishaya 41:13 Ni ne Ubangiji Jehovahnku, Na ƙarfafa ku, na kuwa faɗa muku, 'Kada ku ji tsoro, ni zan taimake ku.' "
Matiyu 28:20 kuna koya musu su kiyaye duk iyakar abin da na umarce ku. Ga shi, ni kuma kullum ina tare da ku har ya zuwa matuƙar zamani."
Yahaya 14:1 "Kada ku damu. Ku gaskata da Jehovah, ku kuma gaskata da ni.
Ishaya 41:14 Ubangiji ya ce, "Isra'ila, ku kima ne marasa ƙarfi kuma, Kada ku ji tsoro, zan taimake ku. Ni Jehovah Mai Tsarki na Isra'ila, ni ne mai fansarku.
Ishaya 43:2 Sa'ad da kuke bi ta cikin ruwa mai zurfi, Zan kasance tare da ku, Wahala ba za ta fi ƙarfinku ba. Sa'ad da kuke bi ta cikin wuta, ba za ku ƙuna

ba, Wuyar da ta same ku ba za ta cuce ku ba.

Zabura 23:1-6 Ubangiji makiyayina ne, Ba zan rasa kome ba. 2 Yana sa ni in huta a saura mai ɗanyar ciyawa, Yana bi da ni a tafkuna masu daɗin ruwa, suna kwance lif. 3 Yana ba ni sabon ƙarfi. Yana bi da ni a hanyar da yake daidai kamar yadda ya alkawarta. 4 Ko da hanyan nan ta bi ta tsakiyar duhu na mutuwa, Ba zan ji tsoro ba, ya Ubangiji, Gama kana tare da ni! Sandanka na makiyayi da kerenka Suna kiyaye lafiyata. 5 Ka shirya mini liyafa Inda maƙiyana duk za su iya ganina, Ka marabce ni, ka shafe kaina da mai, Ka cika tanduna fal da mai. 6 Hakika, alherinka da ƙaunarka Za su kasance tare da ni muddin raina. Haikalinka zai zama gidana har abada.

Yahaya 14:27 Na bar ku da salama. Salamata nake ba ku. Ba kamar yadda duniya take bayarwa nake ba ku ba. Kada ku damu, kada ku ji tsoro.

Filibiyawa 4:7 Ta haka salamar Jehovah, wadda ta fi gaban dukkan fahimta, za ta tsai da zukatanku da tunaninku ga Almasihu Yesu.

Karin Magana 3:24 Ba za ka ji tsoro, sa'ad da kake kwance a gadonka ba, za ka yi ta sharar barci a dukan dare.

Zabura 4:8 Da zarar na kwanta, sai barci ya kwashe ni, Kai kaɗai kake kiyaye ni sosai, ya Ubangiji.

Zabura 33:18 Ubangiji yana kiyaye masu tsoronsa, Waɗanda suke dogara ga madawwamiyar ƙaunarsa.

Romawa 5:2 Ta wurinsa kuma muka sami shiga alherin nan da muke a ciki, saboda bangaskiyarmu, muna kuma taƙama da sa zuciyarmu ga samun ɗaukakar nan ta Jehovah.

Ishaya 55:12 “Za ku fita daga cikin Babila da murna, Za a bi da ku, ku fita daga birnin da salama. Duwatsu da tuddai za su ɓarke da waƙa, Itatuwa za su yi ta sowa don murna!

Yahaya 16:22 Haka ku ma yanzu kuke tare da baƙin ciki, amma zan sāke ganinku, sa'an nan zuciyarku za ta yi fari, ba kuwa mai ɗauke muku farin cikinku.

Luka 12:9 Wanda kuwa ya yi m*sun sanina a gaban mutane, za a yi m*sun saninsa a gaban mala'ikun Jehovah.

Matiyu 10:30 Ai, ko da gashin kanku ma duk a ƙidaye yake.

Ishaya 54:10 Duwatsu da tuddai za su ragargaje, Amma ƙaunar da nake yi miki ba za ta ƙare ba sam. Zan cika alkawarina na salama har abada.” Haka Ubangiji ya faɗa, shi wanda yake ƙaunarki.

Matiyu 11:28-30 Ku zo gare ni dukanku masu wahala, masu fama da kaya, ni kuwa zan hutasshe ku. 29 Ku shiga bautata, ku kuma koya a gare ni, domin ni mai tawali'u ne, marar girmankai, za ku kuwa sami kwanciyar rai. 30 Domin bautata sassauƙa ce, kayana kuma marar nauyi ne.”

Waƙar Waƙoƙi 2:10 Ƙaunataccena ya yi magana da ni. Tashi mu tafi, ƙaunatacciyata, kyakkyawa.

Yusha’u 2:14,19,20 “Don haka, ga shi, zan rarrashe ta, In kai ta cikin jeji, In ba

ta magana. 19 Zan ɗaura aure da ke cikin adalci, Da bisa kan ka'ida, da ƙauna. 20 Zan ɗaura aure da ke cikin aminci, Za ki kuwa sani, ni ne Ubangiji.

Fitowa 3:14 Jehovah kuwa ya ce wa Musa, "NI INA NAN YADDA NAKE," ya kuma ce, "Haka za ka faɗa wa Isra'ilawa, 'NI NE ya aiko ni gare ku.' "

Yusha'u 13:4 Ubangiji ya ce, "Ni ne Ubangiji Jehovahnku Tun daga ƙasar Masar. Banda ni ba ku san wani Jehovah ba, Banda ni kuma ba wani mai ceto.

Yahaya 15:14 Ku aminaina ne in kuna yin abin da na umarce ku.

Wahayin 3:20 Ga ni nan a tsaye a bakin ƙofa, ina ƙwanƙwasawa, kowa ya ji muryata ya buɗe ƙofar, sai in shiga wurinsa, in ci abinci tare da shi, shi kuma tare da ni.

Pastor T. John Franklin
Church of Salvation, Healing, and Deliverance
COS-HAD.org